**SABOBIN FARAWA - Babi na 1-3**

Fara sabuwar shekara ta ba mu damar buƙi na amincin Allah da lura da ƙaunarsa. Lokaci ne na duba shirinsa na ceto mai ban mamaki, farawa da mutanensa na Tsohon Alkawari zuwa ga bayanuwar Yesu a matsayin cika shirin nan domin dukan 'yan adam.

Amma kuma, lokaci ne na bege kamar na almajirai na farko, muna begen ganin Allah a rayuwarmu don mu fahimci ko wanene Yesu da hakkin bayyana wa wasu abin da muka sani.

# Babi na 1 Sabuwar Shekara

**Littafin Firistoci 23:23-25; Zabura 81:1-6**

GABATARWA MINTI 5

**MANUFA:** Domin a waiwaya a kuma yi amfani da zarafin da Allah ya bayar na sabuwar shekara.

Mutum ɗaya ko biyu su faɗi yadda suka yi bukkin sabuwar shekara.

Isra'ila al'umma ce masu noma. Suna yin bukukkuwa a shekara, suna nuna godiya, sabuntuwa, miƙa kansu domin samun ruhaniya daga gun Allah da abin biyan bukata da bukatun da sun shafi ji.

An sa bukkin Busar Kaho a tsakiya dukan bukukkuwa na Isra'ila. Da farko dai buki ne na addini, daga baya ya zama shi ne farkon sabuwar shekara ta Yahudawa (Rosh Hashanah).

Ɗauki lokaci a makon mai zuwa ka karanta Littafin Firistoci 23 duka domin ka gane muhimmancin wannan buki.

TAMBAYOYIN TATTAUNAWA MINTI 20

**Karanta Firistoci 23:23-25**

**Bukkin Busar Ƙaho:**

1. Bukkin Busar Ƙaho:
   a) sau nawa ake yi (aya 24)?
   b) ya kan ɗauki wane tsawon lokaci?
   c) Su wane ne suke yi?

2. Waɗanne abubuwa biyu musamman ake yi a wannan rana (aya 25)? Menene manufar Allah ga mutanensa a wadannan ayyuka? Dubi kuma Farawa 2:2.

3. A tunaninka ina dalilai busa ‹ahonni dukan yini? Lura: wannan ba yakan faru a dukan bukkoki ba.

4. Me ake yi a hadayar da ta shafi amfani da wuta (L. Fir.1:1-3)? Don me ake bukatar irin wannan hadaya yayin da mutane sun taru domin wannan muhimmiyar rana?

CI GABA DA TAMBAYOYI

**Karanta Zabura 81:1-6**
**Raira waƙoƙin yabo ga Ubangiji:**

5. Wace nauwaya ce Allah ya kawar ma Isra'ila (aya 6)?
   Wace damuwa ce "Harshen" Masar ya jawo wa mutane lokacin da suke bauta (aya 5b)?

6. Waɗanne abubuwa marubucin Zabura ya bayyana a wadannan ayoyi kima?
   Waɗanne abubuwa uku game da halayen Allah aka tuna?

7. Don me wannan buki yake da kyau a yi bukin sabuwar shekara?
   Me hankalinmu yake a kai a yau a lokacin bukin sabuwar shekara?

TAKAICIN KOYARWA MINTI 10

An yi bukin Busar Ƙaho a kan rana ta fari ga watan bakwai lokacin da an fara ganin wata. Amma dai wannan ba bukin sabuwar wata ce ko wata sujada ga wata. Wannan hanya ce da Allah ya shirya musamman domin bukin nan inda mutane za su yi sujada ta farin ciki, su matso kusa da Allah ta wurin yin hadayar tsarkakewa.

Wata na bakwai ya nuna ƙarshen girbi tare da duba baya da godiya domin samun amfani mai yawa. Wannan yana shaida cewa a yi shiri domin shuka a lokacin da aka fara samun ruwa - sa bege domin samun biyan bukata daga wurin Allah nan gaba. Isra'ilawa sun gane hakkinsu ga Allah Ubangiji don haka suka taru su yabe shi su kuma yi masa sujada.

Wannan buki ya duba ceton da Allah ya yi musu a Masar yana duba Rana ta yin kafara inda za a kawar da zunubansu musamman. Bukin Busa Îaho yana tuna masu da ceton da aka yi da kuma ceton Isra'ila da za a yi wanda Allahnsu Mai Iko Duka zai yi.

Mutane suna dawowa daga bukin cike da sa zuciya. Bugu da kari, akan kalubalance su da su sake duba rayuwarsu ta ruhaniya da abin da zasu yi ga Allah mai alherin nan.

AIKATAWA MINTI 20

A tattauna na minti 5-7:
Wane irin bukin sabuwar shekara ce ikilisiyarka ta shirya?
Ta wacce hanya ce ta duba baya ta yi godiya domin baiwar ceto da duba gaba domin samun biyan bukata daga gun Allah ta wurin alherinsa?

## SUJADA DA ADDU'A

Karanta Zabura 147:7-11 a matsayin yin sujada. Ka dauki mintoci kima ka yabi Ubangiji domin alherinsa:

- Roƙi mutane uku kowane ya fadi abu ɗaya da zai iya gode wa Allah musamman.
- Roƙi mutane uku kowane ya fadi abin da yana sa zuciya Allah zai yi masa a watanni masu zuwa.

Bayan kowane ya gama fadi, ro‹i mutum ɗaya ya yi addu'a ta godiya.

A rufe da raira waƙar godiya misali:
**Waƙa** "Godiya ga Allah ..."

**HADDACEWA:** Zabura 147:7-11.